Sayyadi Abu Sa'eed Khudri رَضِیَ اللهُ عَنْهُ Ya Ruwaito cewa: Idan Mutum ya farka daga Barci Kullum Safiya Sai Sun Roki Harshe Sunce Masa:, 'Kaji Tsoron Allah عَزَّوَجَلَّ Bisa Abinda ya Shafemu, Domin Mun Tare da kai, Idan Kayi Daidai Muma Muna kan Daidai idan Kuwa ka Kauce hanya Muma Muna na tare !' *(Sunan-e-Tirmizi, Mujallad. 4, Shafi. 183, Hadisi 2415)*

Shahararren Malaminnan na Tafsiri, Mufti Ahmad Yar Khan رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Yace a Daidai Lokacin da yake Fassara Wannan Hadisi cewa : (Ya kai Harshe!) Muna tare da kai Acikin Riba da Faduwa, Jin Dadi da Hutu, Cikin Wahala da Damuwa. Idan Kayi Ba Daida ba Da Kai da mu Duk Munfada a Matsala. Idan kuwa kayi Aiki na Daida Dukkanin mu Zamu samu Girmamawa, Ku Rike Wannan Cewa Harshe Yana Fassara Matsayin Zuciyane.Aiki mai kyau da Rashin Kyau Dukkaninsu Suna zuwane Daga Zucya. *(Mirat, Mujallad. 6, Shafi. 465)*



www.dawateislami.net

## Matsalar da Take Faruwa Idan An Sakarwa Harshe Ragama

Yaku 'Yan uwa na Musulmi ! A wasu Lokutan Sakarwa Harasanmu Ragama yana Jefamu Damuwa mai Yawa sosai. Idan Mutum Yace da Matarsa Na Sakeki, Na sakeki, Na Sakeki Da Harshensa Ga Matarsa da Suke Zaman Aure, Talaaq-e-Mughallazah Ya Faru Kenan. A wani Bangaren kuma ka Iya Jawowa Ayi Kisa ma Miasali Ayi Amfani Da shi wajen Zagi ma Wani Wannan Zai Rura Wutar Gaba da Fushi a Shari'a Baya halatta a Gayawa wani Wata Kalma Marar Dadi Batare da Hakkin Sharia ba Idan Kuma Har Aka Aikata to Hakika anyi Babban Sabo Wanda Ka'iya Kai Mai Yinsa Wuta .

An Ruwaito a Littafin '*Tabarani*' Cewa Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, 'Duk Wanda Ya Shiga Hakkin Musulmi Ya Cutar dashi (Batare da Hakkin Shari'a ba) Hakika Ni Ya Cutar, Wanda Kuma ya Cutar Dani, Ya Sabawa Allah عَزَّوَجَلَّ.'

*(Al-Mu'jam-ul-Awsat, MuJallad. 2, Shafi. 386, Hadisi 3607)*

## Jin Dadi Da Rashin Jin Dadi Na Har Abada

Sayyadi Bilal Bin Haaris رَضِیَ اللہُ عَنْہُ Ruwaito cewa Mnzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace: Mutum Zai Fadi Wani Abu Mai Kyau da Allah Yakeso Batare da yasan Iyakan cewarsa ba Haka Allah Zai yi Farinciki dashi har Ranar Dazasu hadu dashi. Hakanan kuma Wani Mutum Zai Fadi Wata Magana Marar Kyau Ba

Tareda Sanin Iyakancewarta ba Haka Allah عَزَّوَجَلَّ Zai Rubuta masa Fushinsa Gareshi Har Ranar Da Zasu Hadu Dashi. *(Mishkat-ul-Masabih, Mujallad. 2, Shafi. 193, Hadisi 4833; Sunan-ut-Tirmizi, Mujallad. 4, Shafi. 143, Hadissi 2326)*

Shahararren Malamin Tafsirin nan Mai Fatawa, Mufti Ahmad Yar Khan رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Yace Alokacin Dayake Bayanin wannan Hadisi: (Wasu Lokuta Mutum) Zaice wani abu kokuma ya furta wata Kalma Marar Kyau Wacce Zatasa Allah عَزَّوَجَلَّ Yayi fushi dashi na Har Abada. Saboda haka, Mutum ya Lura da Kiyaye me Muke Furtawa da Bakunanmu. Sayyadi 'Alqamah رَضِىَ اللهُ عَنْهُ Yakasance Yana cewa [Akan Hadisin Nan Nasama] Hadisin Bilal Ibn Haaris رَضِىَ اللهُ عَنْهُ Yana Hanani Yin Maganganu Dayawa Idan Nayi Nufin cewa Wani abu Dagan a Tuna da Hadisin nan Sai na fasa Nayi Shiru. *(Mirat, Mujallad. 6, Shafi. 462)*

Yaku 'Yan uwana a Mausukunci! Yin Magana Batare da Tunaniba Kan Jefa Maiyi a Matsala Babba kuma Zata Iya Janyo Fushin Allah عَزَّوَجَلَّ Na Har abada. Hakika Zaman Lfiya da Tsira yana Tattare da Dora Qufl-e-Madinah (Garkuwa da Tsaro) Akan Harasanmu. Yana da Amfani Matuka ka Koyi yin Rubutu alhalin kanason Hra kokuma Nuni da Hannu Maganin Yawan Magana Marar amfani, Yazama halinka Yawan yin Shiru Domin Mai Yawan Magana Kurakurensa zasuyi Yawa Harda Fallasa Sirri, Kuma Zaiyi Wuya a Wajen Irin Wannan Mutane Kasamesu Basa Munafurci da Gulma da Kuma Neman Laifukan Mutane. مَعَاذَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ Wasu



www.dawateislami.net

lokutan Mutum mai Surutu Wasu lokutan har kalmomin da Furtasu Kafircine yake furtawa..

## Makomar Bushashiyar Zuciya

Ubangiji عَزَّوَجَلَّ Ya Gafarta mana Yasa mu dinga Sassauta Harsunanmu, Saboda Shi Harshen Yana Kawo kyekashewar Zuciya, Magana marar Kan Gado da Mancewa da yin Zikrullah. Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace: Using obscene language is from hard-heartedness and hard-heartedness is in fire.

*(Sunan-ut-Tirmizi, vol. 3, pp. 406, Hadees 2016)*

Shahararren malamin Tafsiri Mufti Ahmad Yar Khan رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Yace a lokacin fassara wannan Hadisi: Yana Nufin Idan Mutum ya Amfani da Harshensa ya cire tsoro dukkan abinda yazo bakinsa shi yake fada Na Alheri ko na Sharri Alamace dake nuna Zuciyarsa ta Bushe , Bushewar data raba Jijiyoyinta suka bazu ko ina Har Izuwa Zuciyar itama ta Bushe, Bushashiyar zuciya kuwa Makomarta Gidan WUTA .Ire-Iren Wadannan Mutane Karshensu shine Kafurci Saboda Rashin Girmama Allah عَزَّوَجَلَّ Da Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

*(Mirat-ul-Manajih, Shafi. 641, Mujallad . 6)*

## Datsatsen Harshe !

Ya 'Yan uwana ! A Hakika Abune mai Hadari Yawaita

Surutu marar kan Gado Domin yana iya Bayuwa ka fada Kafurci; مَعَاذَ اللّٰه عَزَّوَجَلَّ. Idan da Mutane Zai zama Halinsu a Koda yaushe yin tunanai kafin furta kowace kalma Sa'an nan da tuna Amfaninta a Ramar Alkiyama Idan kuwa bata da wani Amfani a akiyama barin furta ta shi yafi kawai sai maida Salatin Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم A Gurbin Duk wata Magana marar amfani Anan Duniya da Ranar tashin Kiyama

Yazo acikin *Asraar-ul-Awliya*: Wata Rana Sayyadi Haatim Asam رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه Sai Fadi wata Yashashiyar Magana da Bakinsa mai Albarka. Sai رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه sai danasani Ya kamashi sai ya Datse harshensa ta Tsakanin Hakoransa Har sai da Jini ya dinga Zuba ta Bakin Nasa! Hakakuma shi Wannan bvawan Allah رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Bai kara yin Magana da kowaba [Magana marar amfani]Har tsawon Shekara Ashirin a Madadin Fadar Waccen Magana Marar Kan Gado! *(Asraar-ul-Awliya, Shafi. 33)*

Allah عَزَّوَجَلَّ Yajikansa Yagafarta Mana Domin Alfarmarsu !

اٰمِيْن بِجَاهِ النَّبِيِّ الْاَمِيْن صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم

## Me Mutum Yakamata Yayi Idan Ya Furta Wani Abu Marar Amfani?

Ya 'Yan uwana A Musulunci! Kun fahinci Abinda ya faru akan Sayyadi Haatim Asam رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Tabbas yayi dana sanin yin



www.dawateislami.net

Yashasshiyar Magana Marar amfani Ya Taune Harshensa! Amma fa Alura Musulunci Bai Yadda Kajiwa kanka Rauni ba Kana a Halin Hankali Saboda haka a irin wannan Kissa ta sama Zamu dauka cewa Adaidai Lokacin da Abin Ya faru baya cikin Hayyacinsa , '*Hosh mayn jo na ho woh kya na karay*' ma'ana Idan Mutum bay cikin Hayyacinsa zai iya Aikata komai a Rashin sani '.'

Wata Hallayar kwarai ta Wadannan Waliyyai masu Albarka.Idanda Mutum zaice 'Allah', 'Allah' Sau 12 ko kuma Yiwa Manzon Tsira صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Salati a Maimakon Dukkan Magana Marar Amfani, Ta wannan Hanya Shedan Tabbas Bazai ingizamu furta Maganganu Barkatai ba, Kuma zaiji Tsoron cewa da yayi mana Umarnin Surutun banza Mu kuma sai mu fada yin ZikIrI da Salatin Ga Annabi Dan Gatan Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم!

An Ruwaito a cikinIt *Minhaj-ul-'Aabideen*: Zikiri Yana Shedan Zafi a jiki Kamar yadda mai cutar [Aakilah]. *(Minhaj-ul-'Aabideen, Shafi. 46)*

Aakilah Cutace da take a kan Naman mutum Ta yadda Naman Yake Rabuwa da kashin tana Babbagowa tana barin jikin mai ita..

## Misalai 14 Na Maganganu Marasa Amfani

Abin Takaicine Yanzu, Dawuya Kasamu Abokan Zama na kwarai Mutane da yawa zasu zo maka kamar na kwarai A



www.dawateislami.net

mma kuma Dasu Za'a Yankar maka Baya kuma Da an Zauna sai Maganganu Marasa kan Gado, Idan da idan Mutane suka Hadu sun hadune Domin samun Yardar Allah عَزَّوَجَلَّ. Idan kuma da mutane zasu rabu da Magana marar maana da sun More kuwa a ranar Lahira.

Atuna Cew! Ba Haramun bane yin Yashsshiyar Magana kokuma yinta sabone a'a Ana horone dan Rashin Amfaninta Ga Mai Fadarta da Mai jinta a a kiyayeta kawai *(Ihya-ul-'Uloom, Mujallad. 3, Shafi. 143)*

Daidai lokacin da kake magan marar alfanu akwai kwakwaran zaton Zaka iya yi sabo a Hirarku, Saboda haka Hanya mafi sauki da Nagarta shine yin shiru. Acikn Al'umar mu ta yau Ire-iren Tambayoyin nan har sukansa Mutum jin kunya dan wani lokacin Awajen amsa TYambayar dan kar mutum yaji kunya sai yayi karya, Kuma a lura Mafiya yawa kuma Bugun cikine dan Sanin Yaya kake ciki. Ga Misalan Irin Tambayoyin nan marasa Alfanu, Babu Komai ga Wanda ya Tambayesu da Dalili, Ka Kiyaye irin wannan Tambayoyiko domin kada kasa danuwanka jin kunya kokuma yi maka karya saboda haka a gujesu matukar iyawa. Misali:

1. Menene yake Faruwa!
2. Shin kanayi min Addu'a kuwa a kwanakin nan!
3. Dan uwa ko Kana Fushi Danine ?



www.dawateislami.net

4. Ina Tunanin Kamar Bakaji Dadi ba!
5. Nawa Kasiyo Wannan?
6. Motarka Wacce Kirace [model]?
7. Nawane Tsadar Gidaje a Wajenku?
8. Kayayyaki fa na Zuba Tsada!
9. Yaya Yanayin Gari Yake a Nan kuwa?
10. Kai, Yanayin nan Akwai Zafi!
11. A 'Yan kwankin nan Muna shan Sanyi.
12. Ruwan Saman nan Zai tsaya kuwa!
13. Koda Yaushe Ana Fara Ruwan Sama sai An Dauke Wutar Lantarki!
14. Da'akwai Wutar Lntarki a Wajenku kokuma Babu?

Da Wadannan dama Wasu Tambayoyin da basu da wata alfanu, Ammafa kuma kada Koda yaushe akaji irin Wadannan Tambayoyi Ayi zayo Marar Kyau akan Wanda Yayi Wata kila Ba komaine A Ransa ban a zargin Yafiye Magana Sai yanuwa Mu rabu da aiki da Zato Kuma yin Wadannan Tambayoyi ba Aikin zunubi bane, Watakila shi Mai Tambayar Akwai Abinda yakeso ya sani kuma Kila yana da Kyakyawar niyya a Tambayar dayayi.Kuma bashida Zunubi duk da Yayi Tambayar da ba Dole ceba.



www.dawateislami.net

## Misalin Tambayoyi 13 Da Basuda Mahinmanci Da'akewa Mahajjata[1]

'Yan uwa da Abokai Yawanci sune suke yin Tambatoyi kala-kala ga Dan uwansu Mahajjaci daya Dawo Daga Madinah Ga Misalai 13 :

1. Kasha wahala kuwa A Tafiyar nan?
2. Nasan An Cika sosai ko?!
3. Akwai Tsadar kaya ko?
4. Kasamu Masauki Mai Kyau kokuma Bakasamu ba?
5. Masaukinku a Kusa da Harami Yake ko Nesa Yake da Harami?
6. Yaya Yanayin Gari yake a chan ?
7. Ance Yanayin Zafine a chan ko?
8. Sau Nawa Kakeyin Dawafi a Kowace Rana ?
9. Sau Nawa Kuwa Kayi Umra Kafin Dawowarka?
10. Kayimin Addu'a kuwa a Makkah da Yawa ko Bakayi minba ?
11. Shin Tantinku Yana Kusa da Jamra ne a Mina Ko da Nisa?
12. Kwana nawa Kayi A Madina ?

---

[1] Mataki ko tsani

13. Shin ka Isar da Gaisuwata a Madina kuma Ka Ambaci Sunana kokuwa?

Duk da cewa Bawai an Hana Wadannan Tambayoyi na sama ba, Kayi Tunanin Mahinmancinsu Kafin Kayi dan kada kajefa Alhajin naka Yaji kunya Kokuma kasaka shi yayi Zunubin Karya Abu Mafi kyau shine Idan har Tambayar Bata da Wani Mahinmanci a Hakura Shine Mafi Kyau Domin Yin shiru Gwal ne game wayo'.

## Misalai 4 Na Munanan Kalamai na Sabo

Wasu Mutanen Surutu ne dasu Basa Gujewa Sabo ma a Cikin Zantukansa a irin haka har zargi na karya sukewa Mutane da Basuji ba Basu jiba basu kuma Gani ba Suna maganganu batare da Tantancewa ba Ga Misalin 4 daga ciki:

1. Dukkanin Kauyen mu Gaba day duk masu Barna ne, Ni Kadaine Bana Gulma [Wannan ba Gaskiya Bane sam Saboda ian akabar Dattijai da Mata da Yara wanda zamu iya cewa sun kubuta daga Zarginsa].
2. Dukkanin Maikatan Gwamnati Suna cin Hanci Da Rashawa.
3. Dukkanin Maaikatan [NEPA] Kamfanin Rarraba Wutar Lantarki Mugwayene Mutanene, مَعَاذَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ.
4. Dukkan Maaikacin Gwamnati Barawo ne!



www.dawateislami.net

## Misalin Tambayoyi 19 Marasa Kangado da akeyi a Sallar Layya Eid-ul-Adha

Kadan daga cikin Misalin Tambayoyi Marasa Kangado a Sallar Layya on Eid-ul-Adha:

1. Yaushene zaka siyo Saniyarka?
2. Dabbobi Zasuyi tsada A Wannan ‘yan kwanakin!
3. Nawane Kudin daka Siyo wannan Saniyar?
4. Saniyarka Lafiyayyace !
5. Wannan Saniyar Shekarunta nawa kuwa ?
6. Saniyar nan kuwa tanda Fada ?
7. Amota Aka kawomaka kokuma Korota akayi?
8. Nawa Kabiya Kudin Mota aka kawo maka ita?
9. Sai Yaushe Zaka Yanka Layyaerka ?
10. Mahaucin kuwa Yazo da Wuri ko Ya Makara ?
11. Ana Yankawa Mahaucin Ya tafi sai ya dawo a kurarren Lokaci;.
12. Kayi Gaskiya! Mahauta na batamana lokaci saboda zuwansu a makaree.
13. Naji dadin Kallon Danbarwa Tsakanin Mahauci da Saniya!
14. Na Yarda dakai! cewa wanann Mahaucin Bai Kware ba! (Zai iya zama Cin nama, Zargin karya, mummunan nufi,



www.dawateislami.net

Kuma zai iya  cutar dashi , Hakakuma Babu cutarwa a Bayanin idan Har Mahaucin nan bai iya Aikin nan ba Kuma ta hanyar sanar da wani dan Kubutar da shi Dayake son yasaka wannan Mahauci Aiki.)

15. Shekarar Akuyarka nawa ?
16. Nawa kuwa Ka Siyo Akuyar nan?
17. Kai! Ammafa Anyi maka Tsada.
18. Tana Tafiya kuwa ?
19. Nawa kuwa Kabiya Mahauci Kudin Fida?  Etc., etc.

## Misalai Guda 5 Hira Marar Kangado Alokacin da muke Tadi a Tarho

1. Me kakeyi?
2. Kana Ina?
3. Idan wani ya lira Alhalin wanda aka kira yana Tuka Mota, Ga irin Tambayar da akafi yinta a irin wannan waje,: Wanene Atare da Kai Maiyi maka  Rakiya ?'
4. Ta Ina Ka Wuce?
5. Kuna Ina ? Kunje kuwa ?

Hakika Tambayar da Take da Hujjar yinta Baza'a Kirata da Marar amfaniba, Awasu lokutan Kunyace ma take kama

mutum da zarar an masa ire-iren wadannan Tambayo wasu lokutan har Karya ake saka wanda akayiwa tambayar yayi Misali mutum Bazai iya bayar da Amsar Tambaya 1-2-3-daida ba domin yana son ya ajiye wannan Amsar a matsayin Sirrinsane, Taka maimai yan son ya buye na Me yakeyi ko Shida waye suke Tare ko yana ina zai boye ko domin dalilin tsaro. Jan hankalin na adaina matsawa mutane da tambayoyi marasa amfani nan Duniya da Lahira

## Misalin Tambayoyi 14 Da Suke Tursasa Mutum Yin Karya

Yaku 'yanuwana  a Musulunci!Wasu lokutan Tambaya tana Tursasa wanda akayiwa yayi karya ko domin Gudun jin kunya a wajen fadar Gaskiyar kokuma shi mai tambayar yana da Amsar dayake son ji daga wajen Wanda ya Tambaya ,Toh! Kusani yin Tambayoyin Inakara fada Ba Haram bane Sai dai Duk hanyar da zat jaka ka Sabawa Mahalicci Barinta shine Abinda yafi Ka tseratar da Dan uwanka kar ya aikata Sabon Allah.

Ga Misali 14 Na Ire-Iren Wadan nan Tambayoyi:

1. Ka wahala ne a Wajen Neman Gidanmu ?
2. Kaji Dadin Abincin Da'aka Kawo maka?
3. Yaya kaji Hadin shayin nan?



www.dawateislami.net

4. Yaya kaga Gidanmu Yana da kyau ko?
5. Kanayi min Addu'a ko baka yi?
6. Ya kaji Jawabina [Tunatarwa ta] Dana Gama Yanzu?
7. Ya kaji Zakin Muryata Dana ja Kasida?
8. Kaji haushin abin da na gaya maka?
9. Bakaji dadin Ziyarata ba ko?
10. Nabi duk Na Dameka ko?
11. Na katse maka Hira ko?
12. Kanajin Haushina ko ?
13. Shin na sakaka Farinciki ?
14. Tunda nake na Taba Bata maka Rai

## Kalmomi Masu Hadari kuma Marasa Amfanin Tambayarsu

Wasu Mutane Suna da Ban Mamaki, Suna da Burin Samun Kwarin Gwaiwa Bawani dalili kuna kuma A Duk abinda sukace. Alal Misali:

1. Amma Dai Me Ka Gane ?
2. Kun Lura da Abinda Nace? (Kodayake a wasu lokutan Irin wannan tambayar Tana da Amfani irin nata Musanmman Awajen Malaman Addini ko Mayan

Mutane dake Dangantuwa Ga Addini Suna sane Suke irin wannan tambayar dan Ganin cewa ko an fahimci Darasi kokuma Ba;'a gane ba sai An maimaita kukuma Domin a fadada Bayani Ga Wanda dama shi bai Ganeba sam , A irin wadannan lokuta A Amsa duk da Angane Ba daidai bane tunda acikin Masu daukar Darasin Akwai Wadanda basu gane ba.)

3. Ashe dai Dagaskene ?

4. Ko nayi Kuskure?

5. 'Menene Ra'ayinka ?' Mutum bashi da Zabi lallai Saidai ya Amsa da Tabbatarwa koda kuwa yana da wani zabin bayan wannan kuma ma bai Yarda da abinda mai Tambayar ya Tambaya ba Airin wannan hali, Yin sabo na Karya zai kurdado Ya shigo a irin wannan hali.

Idan kuma Baka da Kwarin Gwiwar Yiwa Mutanen nan Masu Surutun Tsiya Nasiha abu Mafi kyau shine kabar inda suke Domin dukkan amsa musu da kayi da 'A' dan Tabbatar da Abinda Sukace na Sabawa Allah, Wannan Irin Hirar zata iya zamo maka wani aiki da za'a konaka akansa da Wuta! Irin Wadannan mutanen masu Surutun Bagaira ba Sabar har Kalmomin kafirci, مَعَاذَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ suke furtawa a Zantukansu na batarda mutane.

*Ay kash! Zarurat kay siwa kuch bhi na boloon*

*Allah zaban ka ho 'ata Qufl-e-Madinah*



www.dawateislami.net

## Ma'anar Zance Marar Kan Gado'

Idan kalma daya ta isa a isar da sako to kara wata Kalmar ya zama Shirbuci a Magana Saboda babu Bukatarta.

Hujjat-ul-Islam, Sayyadi Imam Muhammad Bin Muhammad Ghazali رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Yace acikin Littafinsa *Ihya-ul-'Uloom*: Idan kalma daya ta isa ya isarda sako (Na mai Magana) Kuma sai yayi Amfani da Kalmomi Biyu, ta biyun Za'a dauketa a Matsayin Shirbuci.Yana Nufin tayi yawan da Ake Bukata a Wannan Wajen, kuma dukkan Kalmar datzo a irin Wannan sigar Abar Jefarwace. *(Ihya-ul-'Uloom, Mujallad . 3, Shafi. 141)*

Idan bukata bata biya ba a kalma kokuma Jumla dayababu laifi a kara wasu kalaman kokuma jumlolin iyakacin Bukata Saboda Haka idan Zancen aka furtashi Fiye da Bukata Yazama Shirbuci kenan, Karin Yakan zamo Karin Jawabine domin kara fito da maganar fili, Kuma misalign karawa murya wani Nau'I na Jan kalmomin da Furtasu ta Hanyar raurawar Murya Wannan Shima Karine Acikin abinda babu bukatar karashi.

Mutane An Rabasu ne Zuwa kashi Uku Gwargwadon Fahimtar su :

1. Masu Basira Sosai
2. Matsakaita a Basira
3. Masu Raunin Basira

Ga Mutane Masu Basira sosai Wani lokaci Kalma daya Kadai a Bayani Zai iya Fahintar ina aka dosa AMMA Mai Matsakaiciyar Fahinta zaiyi wuya ya gane batare da bayani ba Shikuwa mai karancin Basira Sai kayimasa bayani sau Goma kuma yace maka baima san ina aka dosa ba. Saboda wannan Dalili na sama maimaitawa mutumin da dama ya gane ai ya zama bata lokacine kawaai Amma mai Matsakaiciyar Basira Shikuma Bazai Ganeba sai an fadi Kalmomi 12 Zai Gane to yazama anada Bukatrsa kenan kuma barin yin karin anan kuma ba daidai bane.

Hakakuma, Mai karancin Basira bazai gane ba har sai an yi masa Bayani da Kalmomi 100 To kowa kalmomin nan dari bazasu shiga cikin Shirbici ba kokuma kalmomin da ba'a bukatarsu tunda ga wani shi sai anyi sau darine zai gane domin anyi amfani dasune akan dalili. To suma Sau TariKalma daya ta Wadatar akan Cimma wata Manufa amma Sai Ayi ta Magana, Kalma idan tazama bata halal ba to Furta wannan Kalmar ma ba Halal bace .

## Wanda Ya Yarda Da Allah Da Ranar Tashin Kiyama

Bayan Karanta abin da ya Gudana a Sama zaka fahimci cewa zaiyi wuya matuka a kubuta daga Maganganu na shirbici da rashin kan gado, Duk da haka kada ka debe Haso cewa kayita kokari kuma kan Gwada Qufl-e-Madinah A Harshenka (Domin

zama shiru), Kayi Tattaunawa ta haryar Rubutu kokuma Maganar Kurma wato Ta Hanyar Nun babu kalma yin irin wannan kokarin da Zuciya daya Zai sadar damu izuwa Gidan mu na karshe .

A wata Magana ana cewa, 'اَلسَّعْیُ مِنِّی وَالْاِتْمَامُ مِنَ اللّٰہ' shine.Aikina shine yin Kokari Amma cin Ribarsa daga Allah ne ma girma da daukaka عَزَّوَجَلَّ. Ka Haddace wannan Hadisin Na Cikin *Sahih Bukhari* Zai kasance maka mai Amfani sosai wajen Zama Shiru zaizama Halaiyarka, اِنْ شَآءَاللّٰہ عَزَّوَجَلَّ. Manzon Tsira صَلَّی اللّٰہ عَلَیْہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم Yace, 'Wanda Ya Yarda Da Allah عَزَّوَجَلَّ Da Ranar Lahira; Ya Fadi Alheri Kokuma Yayi Shiru.' *(Sahih Bukhari, Mujallad. 4, Shafi. 105, Hadisi 6018)*

## Mutane Masu Surutu Na Ban Mamaki

Idan Halinkane Shiga Kowace Hira Marar Kan gado Mutane kuwa zasu Dinga Saka Mimaita Abin da Kace, Watakila Kaima Ka Taba yiin irin wannan Halaiyyar da Rashin Sani Ka Tuna Yadda kasa wani shima yayita maimaita kansa Misali na yadda za'a maida mutum yayi ta maimaita abin da yace Misali : Zayd Ya gayawa Bakr Wata Magana. Duk da cewa Bakr Ya fahinta Amma sai yayi kamar Baigane ba, Sai ya Dago da kansa da alamar Tambaya, Kuma mafiya yawa wadannan Kalmomi ake Ammafani dasu Kalmomin Tuhuma, sai Yace : Na'am me?



www.dawateislami.net

'Huh?' 'Me Kace?' 'Meye'? Ta Wannan Hanya yasa, Zayd Yayi ta maimaita kalamansa batare da Dalilin yin Hakanba

Tunda Malamin mu Ameer-e-Ahl-e-Sunnat دَامَتْ بَرَكَاتُهُمُ الْعَالِيَه Ya Gane Haka Saboda Yau da Gobe Ya Fahinci Halaiyar Wasu mutane Suna da Halin Saka Kayita maimaita abin da kafada Malam Sai Kawai Yayi Shiru Maimakon ya maimaita Amma daga baya sai agane cewa mai saurаron maganar ashe ya dade da fahintar maganar kawai dai irin halinne da yayi Katutu a Zukatan Mutane kuma Rabuwa da wannan halin a wasu Lokuta Kamar ma bazai yiwu ba cikin sauri Dan kawai Kazo Kaji Wa'azi Guda daya kukuma Ka karanta wasu daga cikin Rubuttukanmu akan wannan fagen Bai isar ba Hanya dayace. Yin tunani mai zurfi kuma ka shirya a Cikin Ranka cewa Daga Yanzu Nadaina Amfani da Kalmomi irin 'eyee 'huh', 'Me', Mekace, da sauransu etc Da Zarar Kaji Wani ya Furta su Koda kuwa kai kamanta Hakan Zai sakaka kayiwa kanka Hisabi.

## Nazarin Tattaunawar

Dear Islamic brothers! Bayanin da ke Bayyana kulawa da aka lura da ita daga wurin Waliyanmu Masu Tsarki رَحِمَهُمُ اللّٰه A lokacin Tattaunawa.

An Anbata Acikin '*Minhaj-ul-'Aabideen*': Wata Rana Sayyadi Fudayl Bin 'Iyaad رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه Ya Hadu da Sayyadi Sufyan Sawri رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه. Dukkanisu Sukayi kuka Bayan Sun Tattauna Daga

nan sai Sayyadi Sufyan Sawri رَحْمَةُ الله عَلَيْه Yace, 'Ya Baban 'Ali (Wannan Alkunyace ta Sayyadi Fudayl)! Inazatan Samun Lada Mai yawa Saboda Haduwata Dakai a Yau,' Sayyadi Fudayl Bin 'Iyaad رَحْمَةُ الله عَلَيْه Yace, Ni kuma Tsoro nakeji Saboda Haduwar nan Tamu.' Sayyadi Sufyan Sawri رَحْمَةُ الله عَلَيْه Ya Tambaya, 'Mai yasa ?' Sayyadi Fudayl رَحْمَةُ الله عَلَيْه Ya Bada Amsa, 'Ba Dukkannin mu Mun Kawata Tattaunawarmu? Ba Dukkanmu Mun Mayar da Tattaunawar mu Ta Zamo Mai Dadi ba?' Bayan y agama saurare, Sayyadi Sufyan Sawri رَحْمَةُ الله عَلَيْه Shima sai yafara Kuka. *(Minhaj-ul-'Aabideen, Shafi. 44)*

Ya Dan uwana a Musulunci. Muyi Tunani Akanta, Wadannan Bayin Allan a Gari Sun hadu da juna ne Domin neman Yardar Allah عَزَّوَجَلَّ. Kuma Tattaunawarsu A kan Tsarin Da Sharia da aje ne Amma duk da Haka Suna cike da Tsoron Allah عَزَّوَجَلَّ Sosai! Dukkanin Wadannan Waliyyai Sun Zubar da Hawaye ne Domin Tsoron Ko Sun Sabawa Allah عَزَّوَجَلَّ Alokacin Tattaunawarsu da Juna, Ko Sun fadawa Juna Wadansu Magaganu Nasu Dadi kokuma sun Fadi wasu Dadadan Kalamai da babu bukatar su! Irin Mutanen nan su kula nasu son nuna zakin Magana Ta hanyar amfani da Karin Magana, Zaurance, Amfani da kalmomi masu wahala ko irin Magana da Larabci, ko fasha [yaren mutanen iran] ko Turanci Alhali suna Tattaunawa da yarenmu na Urdu Amma Saboda su burge Mutane da Ilminsu.



www.dawateislami.net

Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, 'Aranar Tashin Alkiyama, Allah عَزَّوَجَلَّ Ba zai karɓi farilla ko nafila ba daga mutumin da ya ke magana da dabaru [ko Yaudara] da Niyyar jan hankalin mutane ko kuma ya burge su da ita."

*(Sunan Abi Dawood, Mujallad 4, Shafi. 391, Hadisi 5006)*

Babban Malamin Hadisin Nan Muhaddis, 'Allamah Shaykh 'Abdul Haq Muhaddis Dihlvi رَحْمَةُ اللهِ عَلَيْه Yace: 'صَرْفُ الْكَلَام' A nan, a na nufin yin magana ta Karya ko ta hanyar yaudara don sanya tattaunawar ta kasance mai ban sha'awa, da kuma canza ta don haifar da shakku da rashin tabbas.

*(Ashi'a-tul-Lam'aat, Mujallad. 4, Shafi. 66)*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yaku 'yanuwa na a Musulunci! Ku bani damar isar muku da wani Mahinmin Sako akan Mahinmancin Bin Sunnar Manzon Allah da kuma Koyon halaye masu kyau kafin mukawo karshen Wannan Tunatarwa tamu ta yau Mazon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yace, Dukkan wanda Yake son Sunnah ta Yana Sona Kuma duk mutumin da Yake sona Muna tare da shi a Aljannah.' *(Mishkat-ul-Masabih, Mujallad 1, Shafi. 55, Hadisi 175)*

*Seenah tayri Sunnat ka Madinah banay Aqa*
*Jannat may parausi mujhay tum apna banana*

*May my heart be Madinah of your Sunnah, O Beloved*
*In Paradise, grant me a place in your neighbourhood*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب      صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Aduo'i 12 Na Shiga Gida da Fita daga Gida

1. Alokacin Fita Daga Gida Ka Karanta Wannan Addu'a:

بِسْمِ اللّٰهِ تَوَكَّلْتُ عَلَى اللّٰهِ لَا حَوْلَ وَلَا قُوَّةَ اِلَّا بِاللّٰهِ

*Da Sunan Allah عَزَّوَجَلَّ, Na Dogara Ga Allah, Babu Tsimi Babu Dabara Sai Daga Wajen Allah عَزَّوَجَلَّ.*

*(Sunan Abi Dawood, Mujallad 4, Shafi. 420, Hadisi 5095)*

اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ, Domin Albarkar Karanta wannan Addu'a Zaka Kasance akan Hanya Madaidaiciya kuma Za'a Karemaka Dukkan Abin ki da Taimako Daga Allah عَزَّوَجَلَّ.

2. Addu'ar Shiga Gida :

اَللّٰهُمَّ اِنِّيْٓ اَسْاَلُكَ خَيْرَ الْمَوْلَجِ وَ خَيْرَ الْمَخْرَجِ

بِسْمِ اللّٰهِ وَلَجْنَا وَبِسْمِ اللّٰهِ خَرَجْنَا وَعَلَى اللّٰهِ رَبِّنَا تَوَكَّلْنَا

*Ya Allah عَزَّوَجَلَّ! Ina Neman Aherinka Alokacin Shigata daLokacin Fitata Muna Shiga Gida da Sunan Allah عَزَّوَجَلَّ Muna fita Daga gida da Sunan Allah عَزَّوَجَلَّ Kuma a Gareshi muka Dogara Ubangijinmu , Allah عَزَّوَجَلَّ.*

*(Sunan Abi Dawood, Shafi. 420, Mujallad. 4, Hadisi 5096)*

Bayan ka Karanta Wannan Addu'a Sai Kayiwa Mutanen Gidan Sallam Daga nan Kuma sai Kayiwa Annabi صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَالِهٖ وَسَلَّم, Salati Sai kuma Kakaranta sura Surah Al-Ikhlas. Zaka Samu Albarka da Taimakon Allah kuma Gidan Zai Tsira daga Fada Tashin Hankali, اِنْ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ.

3. Kayi Sallama Ga Maharramanka Mata da Maza Sune [Mahaifiya, Mahaifi, Yayye Da Kanne Mata da Maza] A lokacin Shiga da Fita daga gida.

4. Hakakuma Idan Mutum Kawai Ya Shiga Gida Ba Tre da Kiran Sunan Allah عَزَّوَجَلَّ, Ba Misali Batare da Cewa 'بِسْمِ اللّٰه', Ba, Tareda Shedan Suka Shiga Gidan.

5. Idan Kashiga Gidan da Babu Kowa koda Kuwa Gidanka ne Kace

اَلسَّلَامُ عَلَيْنَا وَ عَلٰى عِبَادِ اللّٰهِ الصّٰلِحِيْنَ

*Aminci Akanmu Da Kuma Bayin Allah Na Gargaru*



www.dawateislami.net

Mala'ikun Allah ne Zasu Amsa Wannan Sallamar.

*(Rad-dul-Muhtar, Mujallad. 9, Shafi. 682)*

Tunda Ruhunsa Mai Tsarki Manzon Allah صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم Yana Tareda mu a Gidajenmu mu Musulmi, Zaka iya cewa

اَلسَّلَامُ عَلَيْكَ اَيُّهَا النَّبِيُّ

*Ya Annabi* صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم*! Amincin Allah a Gareka .*

*(Bahar-e-Shari'at, Kashi 16,Shafi. 96; Sharh-ush-Shifa, Mujallad 2, Shafi 118)*

6. Idan zaka Shiga Gidan Mutane Kace When, 'اَلسَّلَامُ عَلَيْكُمْ', Na Shigo?

7. Idan Baabaka Damar Shiga Gidanba Ka Juya da Farinciki Watakila Mazauna Gidan Sun Ki Baka Damar ne Sabida Wani Uzuri daya Sha Kansu.

8. Duk Sanda Aka Kwankwasa Maka Kofa, Sunnane Kace 'Waye? Sa'an nan Mutumin dake Waje Shikuma Zai fadi Sunansa, Misali, '*Muhammad Ilyas*'. Ba Sunnah Bane Kace : '*Madinah!*' '*Nine!*' '*Bude kofar,*' da wasu Misalan Kalmomin a Maimakon Ambatar Suna.



www.dawateislami.net

9. Ka Tsaya nesa da kofar Gidan Zuwa Gefe Daya Bayan Kafadi Sunanka Hakan Zai Hanaka Kallan Cikin Gidan Mutane Da Zarar An Bude Kofar.

10. Bai Hallata ba Yin Leke a Gidan Mutane Wani Lokaci Zaka ga Agaban Gida Akwai Wani Gidan da Yake a dan kasa To Lallai sai An kiyaye Wajen yin Kallo ko tsayuwa a Baranda ko ta Taga Musanman ta Bene Domin Kiyayewa Kar a Dinga Leken Gidan Mutane

11. Idan Kaje Gidan Mutane Bakunta, Kada ka Dinga Kushe Tsarin Yadda Aka Shirya Gidan Domin Mutan Gidan Zasu Iya Jin Huashinka.

12. A sanda Kazo Tafiya Kayiwa Mutanen Gidan Addu'a Ka Gode musu Idan da dama kayi musu Kyauta da Makalolinmu da kanan Littafai kukame DVD na karattukan Yada Sunnah kukuma dai wani abun mai mahimanci.

Domn koyan Sunnah Ta Bangarori da dama Kasayi Littafi Guda Biyu da Maktaba-tul-Madinah Take Bugawa:

1. *Bahar-e-Shari'at,* Kashi 16.
2. Littafin *Sunnatayn aur Adaab*.



www.dawateislami.net

Wata Hanya Daya-Daya Ta Koyan Sunnah Shine Shiga Cikin Tawagar Matafiya ta Madani Qafilahs ta Dawat-e-Islami kuna tare a cikin Masoya Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم

*Seekhnay Sunnatayn Qafilay mayn chalo*
*Lootnay rahmatayn Qafilay mayn chalo*

*Haun gi hal mushkilayn Qafilay mayn chalo*
*Pao gey barakatayn Qafilay mayn chalo*

*To learn Sunan, travel with Madani Qafilah*
*To gain mercies, travel with Madani Qafilah*

*To solve your problems, travel with Madani Qafilah*
*To reap blessings, travel with Madani Qafilah*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب     صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد



www.dawateislami.net

الحمد لله رب العالمين والصلوة والسلام على سيد المرسلين اما بعد فاعوذ بالله من الشيطن الرجيم بسم الله الرحمن الرحيم

## DOMIN ZAMA MUSULMI MAI NAGARTA MAI RIKO DA SALLAH

Tafiyar da dukkan Daren ka a wajen Taron ljtima' Na Dawat-e-Islami , Wanda ake Gabatarwa Duk Ranar Alhamis Bayan Sallar Maghrib a Garinku ,Domin Neman Yardar Allah عزوجل Tareda kulla Niyyar koyon Sunnoni . Mayar dashi Halinka tafiya cikin tawagar Madani Qafilah kwana 3 a Duk Farkon Watan Musulumci Tareda Masoya Ma'aiki , Tareda cike Katin Madani In'amaat a kullum domin samun Fikr-e-Madinah Tareda Bayarda shi ga Wanda ya dace daga cikin 'Yan uwa Wanda Alhakin Karba yake Kansa a Garinku kwana Goman Farkon Watan Musulumci.

Manufar mu itace: 'Zamuyi kokarin sauya kawunan mu da mutanen Duniya ان شاء الله عزوجل Domin sauya kawunan mu , Sai Muna Amfani da Katinmu na Madani In'amaat San Nan kuma Kokarin kawo sauyi ga Mutanen Duniya Sai Muna shiga cikin Tawagar Matafiya Madani Qafilahs ان شاء الله عزوجل

MADANI CHANNEL

DAWAT-E-ISLAMI

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagaran
Purani Sabzi Mandi, Karachi, Pakistan
UAN: +92 21 111 25 26 92 | Ext: 7213
Web: www.maktabatulmadinah.com | E-mail: feedback@maktabatulmadinah.com